Wayyo, Wayyo, Wannan tsantantsar ribace, kada kayi, kuam sai dai idan kanason ka saya to ka siyar da dabinonka da wani cinikin daban, sannan ka saya da kudin

Daga Abu Sa'id Alkhudri -Allah yarda da shi- :Bilal ya zo wajen Annabi da Dabino Birni, sai Annabi ya ce da shi "ina ka samo wannan? Sai Bilal ya ce: ya kasance Muna da Dabino ne Mara kyau sai na saida shi da kwano biyu da kuma daya don in ciyar da Annabi sai Annabi yace lokacin:m "Wayyo, Wayyo, Wannan tsantantsar ribace, kada kayi, kuam sai dai idan kanason ka saya to ka siyar da dabinonka da wani cinikin daban, sannan ka saya da kudin"

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Bilal ya zo wajen Annabi da Dabino Biryani mai kyau, sai Annabi yayi mamakin kyawun kansa kuma ya ce: Daga ina wannan? sai Bilal ya ce: ina da wani Dabino ne, sai na bada kwano biyu na mara kyau aka bani kwano daya na wannan mai kyau, don ya kasance na kawowa Annanbi daga cikinsa, sai hakan ya girmama ga Annabi kuma yayi kash da hakan, domin hakan Sabo ne a wajensa kuma shi ne Mafi girman Musibu, kuma ya ce: wannan aikin naka, shi ne tsantsan Riba wacce aka haramta, to kada kayi hakan, sai dai idan kanaso sai ka canza mara kyawun da kudi ta hanyar siyarwa, sannan kudin sai ka siyi Dabinon da shi mai kyau, to wannan hanya ita halas ce kana iya yinta, don nisantar fadawa cikin haramun. "Taisir Allam Sharhin Umdatu Al'ahkam" (Shafi/568)

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/6033